# IMANI DA MUSLUNCI

Fassarar:
**Mallam Yahya**

Turkanchi:
**Hüseyn Hilmi Işık**



# IMANI DA MUSLUNCI

Fassarar:
**Mallam Yahya**

Turkanchi:
**Hüseyn Hilmi Işık**

**Printing**

Çınar Matbaacılık

Yüzyıl Mah. Matbaacılar Cad. Atahan No: 34 Kat: 5

Bağcılar - İSTANBUL - TURKEY

Sertifika No : 45103

Tel: (0212) 628 96 00

**www.hakikatbooks.com**

# ZAMKATIMU

# IMANI DA MUSLUNCI
## MAWALLAFI MAULANA DIYAUDDIN SHEIKH KHALID ALBAGHDADI (Allah Yajı ƙanshı da rahama )

Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin Ƙai

# GABATARWA
## Da Sunan Alla Mai Rahama Mai Jin ƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai, Tsira da Amincin Allah su tabbata ga Annabi Muhammad, da iyalan gidansa, da sahabbansa. Bayan haka, wannan ɗan ƙaramin littafi mai suna **(IMANI DA MUSLUNCI)** wanda ya ƙunshı abubuwa da yawa game da addının Musluncı. Manzon Allah SAW ya na cewa: (mafificınku shine wanda ya san Ƙur'ani kuma ya koyar) ya ƙunshi fatawowi game da Azumin Ramadhan, mai Albarka, wanda yayi a yayin karɓa tambayoyi da suka shafi wannan babbar ibadah mai muhimmanci. An yanke shawarar maida wannan aiki zuwa littafi saboda bukatar dake akwai cewar mutanen da basu samu halartar darasin ba su samu gamsassun amsoshi da suka ƙunshi hukunce hukunce, na wannan azumi da abubuwan dake cikinsa kamar Sallar Asham/Tahajjud, I'tikafi, lailatul Qadri, da kuma Zakatul Fiɗri. Kuma Mallam yayi ƙoƙarin bada amsoshi bisa gwargwadon fahimtarsa da koyarwar littafin Allah, sunnar Manzonsa (S.A.W) da fahimtar magabata na ƙwarai. Da fatan Allah ya kyautata niyyarmu, kuma ya sanya wannan aiki ya zama karɓaɓɓe a wurinsa. Sannan ya yafe kura kuran dake akwai a ciki.

**Tambaya:** WANE IRIN ALBISHIR MANZON ALLAH YAKE YIWA SAHABBANSA KAFIN AZUMI?

**Amsa**:- Ya tabbata wajen Manzon Allah (S.A.W.) ya kasance yana yiwa sahabbansa bushara zuwan Ramadan yana basu labarin cewar a cikin watan Ramadan ana buɗe ƙofofin Rahama da ƙofofin Aljanna, kuma ana rufe Jahannama, sannan ana ɗaure shaiɗanu, kamar yadda yazo a hadisin Abi Huraira (Sahihul bukhari, hadisi na 1899).

**Tambaya:** YAUSHE NE WATAN RAMADAN YAKE TABBATA?

**Amsa**:- Watan Ramadan yana tabbata ne da zarar anga jinjirin watan ko cikar watan Sha'aban kwana talatin. Domin hadisi ya tabbata daga Abi Huraira yace Manzon Allah (S.A.W.) ya ce" kuyi azumi domin ganin wata,

kuma ku sha ruwa domin ganinsa. Idan kuma wata ya faku a gareku to ku cika Sha'aban kwana talatin".

**Tambaya:** SHIN ZA A IYA AMFANI DA ƘIRGEN KALANDA KO LISSAFIN TAURARI WAJEN TABBATAR DA WATAN RAMADAN?

**Amsa**:- Ɗaukar Azumi akan lissafin kalanda ko lissafin taurari bidi'a ne domin haka bai tabbata ba daga bakin Manzon Allah (S.A.W.) ko magabata, ko ijima'in malamai (duba fatawa na Ibn Taimiyya).

**Tambaya:** SHIN WATA SAI KOWA YA GANSHI NE SANNAN A ƊAUKI AZUMI KO KUWA?

**Amsa**:- Ana iya ɗaukar Azumi ko da mutum ɗaya ne yaga wata. Domin hadisi ya tabbata daga Abdullahi dan Umair (R.A.) yace Mutane sun rigen ganin jinjirin wata sai na gayawa Manzon Allah (S.A.W.) cewar ni na ganshi sai Manzon Allah (S.A.W.) yace: "suyi azumi (duba Abu Dauda 2340, Hakim da Ibn Hibban suka ingantashi, Hakim 423 Ibn Hibban 3438). Amma mafi yawan malamai sun ce ganin lallai mutumin ɗaya ga watan ya zamanto adali watau wanda ba zai yi ƙarya ba.

**Tambaya:** SHIN IDAN ANGA JINJIRIN WATA A WATA ƘASA, MUTANEN DAKE A WATA ƘASA DABAN SUMA ZASU ƊAUKI AZUMI?

**Amsa**:- Hadisin Manzon Allah (S.A.W.) ya tabbata cewa ko ina aka ga wata ya shafi dukkan Musulmi ne gaba ɗaya. Domin Manzon Allah (S.A.W.) yace idan kunga jinjirin wata, to ku azumceshi idan kun ganshi kuma to ku buɗe bakinku (Bukhari babi na sha ɗaya Kitabus-Siyam). Idan kun gani anan yana nufin alummarsa gaba ɗaya. Amma akwai saɓanin malamai akan mafitar wata, wasu sun ce ana iya ganinsa a wani wuri kamar Najeriya amma ba a ganshi a Saudiyya ba don haka wasu malamai suka ce kowane gari ya dogara da ganin watansa amma mu mun runjayar da mun rinjaya akan maganar Manzon Allah cewa a wuri ɗaya ya wadatar ga dukkan alummar Musulmi. Dalilin "faɗar Allah Maɗaukakin Sarki "Zaa tambayeka game da jinjirin wata, kace masu shi lokutane ga mutane da Hajji. Kuma ba a taɓa jin waɗansu mutane sun ce zasu yi amfani da ganin watansu ba daban wajen zuwa Hajji.

**Tambaya:** MENENE MA'ANAR AZUMI?

**Amsa**:- Ma'anar azumi a Sharia shine kamewa daga dukkan abubuwan da suke ɓata azumi kamar ci da sha, jima'i da sauransu daga fitowar alfijir zuwa faɗuwar rana da niyyar bautawa Allah.

**Tambaya:** MENENE DALILIN WAJIBCIN AZUMI?

**Amsa**:- Daliln wajibcin azumi shine faɗar Allah Maɗaukaki "ya ku waɗanda kukayi imani an wajabta muku yin azumi kamar yadda aka wajabtawa waɗanda suka gabaceku ko kunji tsoron Allah. Kwanaki ne ƙididdigaggu" Kuma hadisin daya gabata na Abi Huraira ya nuna wajibcin domin Manzon Allah (S.A.W.) ya ce kuyi azumi idan kun ganshi. wannan kuwa umarni ne.

**Tambaya:** SU WANENE AZUMI YA WAJABA A GARESU?

**Amsa**:- Azumin Ramadan ya wajaba akan dukkan Musulmi baligi mai hankali kuma wanda yake da ikon yi, sannan mazaunin gida ba matafiya ba. Amma azumi baya wajaba akan waɗannan.

1. Kafiri[1]:- Azumi baya wajaba akansa, hakanan ramuwa bata wajaba a kansa idan ya musulunta a gaba.

2. Yaro:- wanda bai balaga ba. Amma za a umarceshi domin ya saba kamar yadda magabata suke yiwa 'ya'yansu.

3. Mahaukaci:- Azumi bai wajaba a kansa ba. Dalili kuwa Manzon Allah yace an daga alƙalami akan mutum uku wanda mahaukaci da yaro na cikin ukun daya ambata saboda haka idan mahaukaci sai ya rama azumi to yaro ma kenan zai rama azumin da ya sha idan ya balaga. Haka ma mai bacci da yayi jima'i saboda haka malaman da suka ce mahaukaci ya rama azumi basu da wata madogara daga Alƙu'ani ko maganar Manzon Allah (S.A.W.).

4. Wanda ya gaza yin azumi saboda tsufa zai sha azumi kuma ba zai rama ba sai dai zai ciyar.

5. Mara lafiya wanda ba zai iya azumi ba to shi zai rama bayan ya warke. Amma cutar da ake tabbatar bazata warke ba, to wannan ma zai riƙa ciyarwa.

6. Matafiyi:- Azumi bai wajaba a kansa ba amma zai rama.

7. Mai haila to jinin biƙi:- baza su yi azumi ba, amma zasu rama.

**Tambaya:** YAUSHE NE AKE ƊAUKAR NIYYAR AZUMI?

**Amsa**:- Ana ɗaukar niyyar azumi ne kafin ketowar alfijir idan ya kasance azumin farilla ne, domin faɗar Manzon Allah (S.A.W.) wanda bai ɗauki niyyar azumi da dare ba (kafin ketowar alfijir) baya da azumi" Nana Hafsa ta ruwaitoshi (R.A.) Sheikh Albani yayi tahaƙiƙinsa a sahihu jamiu

(1) Jalaluddın Rumı 22

Sagir lamba na 6535 ko kuma sahihin NisaI, tahaƙiƙin .

**Tambaya:** YAUSHE NE LOKACIN BUƊA BAKI (SHAN RUWA)

**Amsa**:- Buɗa baki yana tabbata ne da zaran rana ta faɗi ko da mutum yayi buɗa baki ko bai yi ba. Dalili kuwa shine, hadisin Abdullahi Ibn Awfa yace mun kasance cikin tafiya tare da Manzon Allah {S.A.W.} alhalin cewa yana azumi, yayin da rana ta faɗi sai yace wa wani daga cikin sashen sahabbansa ya kai wane ka tashi ka shirya mana abin buɗa baki (farau-farau) sai yace ya Manzon Allah ina ma mun ƙara yammata (shin yana kokwanton faɗuwar rana ne) sai yace ka sauka ka shirya mana abin buɗa baki sai yace ya Manzon Allah ina ma mun ƙara yammata sai yace ka sauka ka shirya mana abin buɗa baki sai yace ya Manzon Allah ai akwai sauran rana sai yace ka sauka ka shirya mana abin buɗa baki sai ya sauka sai ya shirya musu sai Annabi {S.A.W.} yasha ruwa sannan yace idan kuka ga dare ya gabato daga nan hakika mai azumi ya buɗe baki (ana nufin ko yasha ruwa, ko bai sha ba) (Bukhari 1958 Kitabussiyam) kuma ya tabbata a cikin Bukhari daga Sahal ibn Saad Yace hakika Manzon Allah (S.A.W.) yace mutane baza su gushe cikin Alkhairi ba, matukar suna gaggauta buɗ baki. Amma abin mamaki a yanzu sai kaga mutane sun yi salla ba su sha ruwa ba, ko kuwa su bari har sai taurari sun bayyana, sannan su yi buɗe baki, tsammanin su yin haka shine dai-dai, alhali yin hakan ya saɓa ma sunna kamar yadda ya tabbata a hadisin da ya gabata.

**Tambaya:** YAUSHE NE YAFI DACEWAAYI SAHUR?

**Amsa**:- A sunnace ana so a Jinkirta yin sahur zuwa kusan ketowar Alfijir. Hadisi ya tabbata daga Anas ɗan Malik, daga Zaid bin Thabit (R.A.) yace "Mun ci Sahur tare da Manzon Allah (S.A.W.) bayan wannan sai Manzon Allah (S.A.W.) ya tashi zuwa sallah. Sai Anas ya tambayi Zaid bin Thabit minene tsakanin cin sahur da yin sallar Asuba? Sai ya ce gwargwadon Aya 50 (watau mutum ya karanta Aya 50)". (Bukhari, 1921, muslim 1097). Akwai kuma hadisin Sahl ibn Saad yace:- "Na kasance ina yin sahur cikin iyalina bayan wannan sai in yi gaggawa domin samu Sujada (Sallah) da Manzon Allah (S.A.W.)". Wannan ya nuna cewa ana yin sahur ne dab da ketowar Alfijir (Bukhari, 1920).

**Tambaya:** IDAN MUTUM YANA CIKIN SHAN ABIN SHANSA LOKACIN SAHUR SAI YAJI KIRAN SALLAH YAYA ZAI YI?

**Amsa**:- Anan mutum zai karasa abin shansa ne. Domin hadisi ya tabbata daga Abi Hurairata (R.A.) yace:- Manzon Allah (S.A.W.) yace:

“Idan dayan ku yaji kiran Sallah alhali kwarya tana hannunsa kada ya ajiye ta har sai ya biya bukatar sa (sai ya gama sha)”. (Abi Dauda ya rawaito shi, Babi na 18, hadisi na 2060) Hadisin Sahihi ne, kuma Sheikh Albani ya ingantashi a cikin Sharhin Abi Dauda hadisi na 1350. Amma mutane suyi hattara kada su mai da wannan ya zama Al’adar su kullum.

**Tambaya:** MENENE BAMBANCI TSAKANIN AZUMINMU DA AZUMIN YAHUDU DA NASARA?

**Amsa**:- Bambancin Azumin Alummar Annabi Muhammad (S.A.W.) da na Yahudu da Nasara shine yin sahur da gaggauta buɗe baki. Hakika Manzon Allah (S.A.W.) ya faɗa a cikin hadisin Amr bin Ass (R.A.) yace:- Abin da yake bambanta Azuminmu dana mazowa littafi shine cin sahur (Abi Dauda 2059, Muslim) Sheikh Albani ya ingantashi.

**Tambaya:** MENENE FALALAR YIN SAHUR

**Amsa**:- Hadisi ya tabbata daga Anas dan Malik (R.A.) yace:- Hakika Manzon Allah (S.A.W.) yace Kuyi sahur, hakika yin sahur akwai albarka a cikinsa.(Bukhari 1923) saboda haka duk abin da Manzon Allah ya ambace shi da Albarka mutum zai yi wasa da shi kuwa?

T**ambaya:** DAME AKAFI SO MUTUM YA FARA BUƊA BAKI?

**Amsa**:- An fiso ya fara buɗa baki da ɗanyen dabino, idan har bai samu ba sai yayi da busasshe, idan bai samu ba sai yasha ruwa. Dukkan wannan zai zama kafin yayi sallah ne, kuma an fiso yayi shine a mara (1,3,5,7,9,..).Domin hadisi ya tabbata daga Anas dan Malik (R.A) yace manzon Allah (S.A.W) ya kasance yana buɗe baki da ɗanyen dabino kafin yayi sallah, idan bai samu ɗanye ba, ya kanyi da busasshe, idan kuma bai samu busasshe ba sai ya kamfaci ruwa yasha.(Abi Dauda, Babin Buɗe Baki,2065). Hadisi ne ingatacce.

T**ambaya:** WACCE ADDUA CE TA TABBATA DAGA MANZON ALLAH (S.A.W) YAYIN BUƊA BAKI ?

**Amsa**:- Abdullahi ɗan Umar yace:- Manzon Allah (S.A.W) ya kasance idan ya buɗe baki sai yace “Ƙishin ruwa ta tafi jijiyoyi sun jike, lada ta tabbata in Allah ya yarda”.

Hadisi ne Hassan idan aka haɗa hanyoyinsa (Sheikh Albani ya ingatashi a tahaƙiƙinsa na Dauda, Hadisi na 2066) amma mutum zai iya ƙarawa da roƙon Allah akan bukatunsa na duniya da lahira bayan yayi wannan Adduar.

**Tambaya:**YAUSHE NE YA KAMATA AYI ADDUAR BUƊA BAKI?

**Amsa**:-Ana yin Adduar buɗa baki ne da zarar mutum ya sha ruwa saboda hadisin daya gabata na Abdullahi bin Umar yace manzon Allah (S.A.W) yanayin Adduar ne bayan ya sha ruwa (buɗa-baki).

**Tambaya:** MENENE FALALAR WATAN RAMADAN?

**Amsa**:- Azumin Ramadan yana da falaloli da ywa. Daga cikin falalar azumin sun hada da:-

a. Yana kankare zunubin mutum kamar yadda yazo a hadisin Khuzaifah (R.A.) Manzon Allah {S.A.W} yace "fitinar mutum a cikin iyalansa, da dukiyarsa ko maƙwabcinsa sallah da azumi da sadaka suna kankaresu". (Bukhari).

b. Yazo a hadisi, dukkan aikin Ɗan Adam nasa ne Malaiku suke rubuta shi, amma azumi wannan na Allah ne Shi Yake saka shi (hadisin ya tabbata a targhib wattarhib, juzI na farko shafi na 75).

c. Hadisi kuma ya tabbata daga Jabir ɗan Abdullahi (R.A.) daga Manzon Allah {S.A.W.} cewar azumi garkuwane ga ɗan Adam zai yi garkuwa dashi daga wuta. sannan hadisi ya tabbata daga Muazu dan Jabal (R.A.) cewa hakika Manzon Allah {S.A.W.} yace dashi shin bazan nuna maka ƙofofin alheriba? Sai yace naam ya Rasulullah sai yace azumi garkuwa ne kuma akwai hadisin Abi Umamata (R.A.) yace, "Nace wa Manzon Allah ka umarceni da wani aiki da Allah Zai amfanar dani dashi sai yace ka lizimci azumi domin babu kamarsa" (dukkan waɗanna hadisai sun tabbata a targhib, tahaƙiƙin Sheikh Albani juzui na farko shafi na 578).

d. Azumi kuma shine sababin tsoron Allah.

e. A lokacin azumin Ramadan ana buɗe ƙofofin Aljanna, kuma ana kulle ƙofofin Jahannama sannan a ɗaure shaiɗanu kamar yadda ya tabbata a hadisin Abi Huraira (Bukhari, 1899).

f. Hadisi ya tabbata wanda Imam Tirmizi ya ruwaito cewar Manzon Allah {S.A.W.} yace "Bashin bakin mai azumi yafi ƙamshi fiye da turaren miski a wurin Allah" hadisine sahihi. Sannan wani hadisin ya tabbata daga Sahl bin Saad (R.A) daga Manzon Allah {S.A.W.) yace a cikin Aljanna akwai wata kofa ana kiranta Rayyanu, masu azumi zasu shigeta ranar tashin kiyama, babu wanda zai shigeta sai su. Idan sun shiga sai a kulleta babu wanda zai sake shiga (Bukhari 1896) Tirmizi ya kara bayani a cikin riwayarsa cewar wanda ya shigeta bazai ji ƙishin ruwa ba har abada.

**Tambaya:** MENENE MAFIFICIN AIKIN DA MAI AZUMI ZAI YI?

**Amsa**:- Aikin da yafi falala ga mai azumi shine

1. Karatun Alƙur'ani, ma'ana ya lazince shi dare da rana, kuma ya dinga izna da abin da yake karantawa. Amma idan bazai iya karatun Alƙur'ani ba, to sai ya rinka lazimtar inda ake karatun Alƙur'ani ko fassara shi domin hadisi ya tabbata daga nana Fadima da Abu Huraira yardar Allah ta tabbata a garesu sun ce:

"Mala'ika Jibrilu ya kasance yana bijirowa da Annabi (S.A.W.) Alƙur'ani sau ɗaya a kowace shekara, sai ya bijiro masa dashi sau biyu a shekarar da zai yi wafati. Bukhari da Muslim ne suka ruwaito[(2)].

Wannan yana nuna cewa karatun Alƙur'ani shine mafificin ibada a cikin watan Ramadhan.

Allah maɗaukakin Sarki yace, "Lallai mun saukar dashi a daren Lailatul Kadari[(3)](1).

2. Kyauta: Ya kamata mai Azumi ya yawaita kyauta wajen ciyar da jama'a, da sadaka, da taimakon gajiyayyu da makusanta. Kamar yadda ya tabbata a hadisin ibn Abbas cewa: "Annabi (S.A.W.) ya fi kowa kyauta, kuma mafi alkhairinsa yana yinsa ne a Ramadhan yayin da yake saduwa da Jibrilu. Kuma ibn Abbas (R.A) yace Alkhairin Manzon Allah (SAW) yafi sakakkiyar iska". Bukhari ne ya ruwaito shi[(4)].

3. Nafil fili: Ana so mai Azumi ya yawaita Nafil Fili musamman ƙiyamul laili, saboda hadisin Abu Hurairah yardar Allah ta kara tabbata a gareshi yace: Manzon Allah (S.A.W) yace: "Duk wanda ya tsaya ƙiyamulaili yana mai imani, da neman lada; an gafarta masa zunubansa da suka gabata". Bukhari ne ya ruwaito shi[(5)].

Haka kuma Manzon Allah (S.A.W) yace: Wanda yayi sallah dare tare da liman har yagama za'a rubuta masa ladan ƙiyamullaili[(6)].

Kuma an fi son duk wanda zai yi ƙiyamullaili ya tsawaita tsayuwar saboda hadisin Khuzaifa (R.A) yace:

"Manzon Allah (S.A.W) ya kasance yana tsawaita karatu a sallar dare a watan Ramadhan fiye da sauran sallolin dare, yace: Manzon Allah (S.A.W) yakan karanta Suratul Bakarah da Nisa'i da Ali'Imran a raka'a ɗaya, kuma

---

(2) Bukhari K = 66, B = 7, H = 4998 da Muslim K = 44, B = 15, H = 2450.

(3) Suratul Kadari Aya 1

(4) Bukhari K = 1, B = 5, da Muslim K = 43, B = 12, H = 2308.

(5) Bukhari K = 31, B = 70, H = 2009, da Muslim K = 6, B = 25, H = 760.

(6) Targib Wattarhib wanda Albani yayi wa tahƙiƙi lamba (1078).

baya wuce ayar da akayi tsoratarwa a cikin ta sai ya tsaya ya roƙi Ubangiji tsari. Kuma bai gama raka'a biyu ba sai ga Bilalu (R.A) yazo yana neman izni ayi sallar Asuba. Ahmad ya ruwaito wannan hadisin kuma ya ingantashi.

4. Yawan Zikiri da Salatin Annabi (S.A.W): Abune mai matuƙar falala mutum ya yawaita Zikiri da Salati ga Shugaban Halitta irin wanda ya tabbata daga bakin Manzon Allah (S.A.W).

5. Ciyar da mai Azumi abin Buɗa baki: Yana daga cikin mafificiyar ibada mutum yayi ƙoƙari wajen bawa ɗan uwansa abin Buɗe baki saboda hadisin da Annabi (S.A. W) yake cewa: "Duk wanda ya ciyar da mai Azumi abin da zai yi bude baki yana da kwatankwacin ladan wanda ya ciyar batare da an rage ladan wanda ya ciyar ba". Tirmizi yace wannan hadisi ne hasanun sahih(1).

6. Umrah: Yin Umrah a cikin watan Ramadhan ga wanda Allah ya bashi iko yana daga cikin Aiyukan da ake kwaɗaitar da mai Azumi yayi. Amma duk da haka bai kamata mutum yatafi Umrah ya bar makwabtansa da danginsa da sauran mabukata a cikin yunwa da halin ƙaƙani kayi ba. Kuma ya kamata mu fahimci cewa, ciyarwa itace abinda Annabi (S.A.W) yafi ba muhimmanci a ckin watan Ramadhan.

**Tambaya:** WAƊANNE HALAYE YA KAMATA MAI AZUMI YA LAZUMTA?

**Amsa:**- 1. HAƘURI: Ya kamata mai Azumi ya lizimci hakƙuri, domin shine zai hana mutum bin soye soyen zuciyar sa, kuma shine zai bashi juriyar bin umarnin Allah. Hadisi ya tabbata daga Manzon Allah (S.A.W) cewa: "Idan dayanku ya kasance yana Azumi, kada yayi maganganun fasiƙanci ko rafasu, kuma idan wani ya zage shi ko ya yake shi yace: Ni Azumi nake". Bukhari ne da Muslim suka ruwaito(7).

2. RIƘON AMANA: Ya kamata mai Azumi ya kasance mai riƙon amana, domin riƙon amana zai taimaka masa wajen bada haƙƙokin da Allah ya umarce shi ya bayar.

Anan ya zama wajibi mu jawo hankalin waɗansu daga cikin 'yan kasuwa waɗanda suke amfani da watan Ramadhan wajen cutar da al umma wajen tsawwala farashin kayayyakin masarufi, da kuma yin algus ko yaudara a cikin ciniki, domin duk abinda aka samu ta hanyar haram shi zai sa cinsu da shansu da tufafinsu ya zama haram. Kuma wannan shi zai sa Allah yaƙi karɓar Addu'arsu.

(7) Bukhari K = 30, B = 2, H = 1894 da Muslim K = 13, B = 29, H = 1151

Anan ma muna ƙara jawo hankalin shugabanni waɗanda Allah ya danƙa dukiyar Al'umma a hannunsu da su ji tsoron Allah su riƙe Amana, kada su dinga ɗiban dukiyar al'umma suna yin Umrah ko kuma su biya wa wasu mutane, domin Allah baya karɓar ibadar da akayi da dukiyar haram.

3. RAHAMA: Ana son mai Azumi ya zama mai jin ƙai, karimi, mai yalwar zuciya da hannu, kuma mai son biyan bukatar Al'ummah gwargwadon hali. Domin Manzon Allah (S.A.W) yace: "Duk wanda ya ciyar da mai azumi yana da kwatankwacin ladan wanda ya ciyar ba tare da an rage ladan wanda aka ciyar ɗin ba".

4. NASIHA: Ya kamata mai Azumi ya zama mai nasiha wajen hana munkari da umarni da kyakkyawan aiki.

5. SULHU: Ya kamata mai Azumi ya zama mai yin sulhu a tsakanin mutanen da basa ga maciji, musamman tsakanin dangi, domin ya tabbata cewa: ƙiyayya tana hana karɓar ibada da addu'a, har sai masu adawar sunyi sulhu a tsakaninsu.

6. RINTSE IDO DA KAME FARJI: Ya kamata mai Azumi ya rintse idonsa ya kuma kame farjinsa daga dukkanin abinda Allah ya hana, musamman kallon matan mutane, da zina.

7. KAME HARSHE: Ya kamata mai Azumi ya kame harshensa daga giba (yi da mutane) da zagin mutane da cutar dasu da ƙarya wacce ta zama ruwan dare a tsakanin al'ummah.

8. IKHLASI: Ya kamata duk mai azumi yayi domin neman yardar Allah, ba don mutane su yabe shi ba, kada kuma yayi don Allah da waninsa.

Anan muna jan hankalin yan uwa masu bada sadaka ko ciyar da masu Azumi da masu tafsirin Alƙur'ani mai girma, da masu zuwa Umrah, da limamai masu rera tilawa a sallar tarawihi, da masu sauran aiyuka na gari da su rinka yi domin neman yardar Allah.

9. BIN SUNNAR MANZON ALLAH: Ya kamata mai Azumi ya rinka koyi da sunnar Manzon Allah (S.A.W) sau da kafa a duk ibadar da zai yi. Ya kuma nisanci dukkanin bidi'o'i, musamman bidi'o'in da ake yin su a cikin watan Ramadhan, kamar nafil fili da falaloli da ake bayarwa waɗanda basu tabbata daga manzon Allah (S.A.W) ba, ko magabata nagari.

10. TARBIYYAH: Ya kamata mai Azumi ya kula da tarbiyar gidansa musamman kangararrun yara waɗanda basa Azumi ko kuma masu shaye shaye.

Kuma ya kamata iyaye su yawaita yiwa 'ya'yansu addu'a, a cikin watan Azumi, domin Allah ya shiryesu.

**Tambaya:** YAUSHE AKE FARA SALLAR ASHAM?

**Amsa**:- Ana fara sallar Asham a daren da aka ga watan Ramadhan, domin wannan daren daren Ramadhana ne.

**Tambaya:** RAKA'A NAWA AKE YI A SALLAR ASAHAM?

**Amsa**:- Raka'oi goma sha daya ne suka tabbata daga Manzon Allah (SAW). Waɗannan raka'oin sun haɗa harda Wutiri. Domin hadisi ya tabbata a cikin Bukhari, yayin da aka tambayi Nana Ai'sha radiyallahu anha, yaya sallar Annabi (S.A.W) take a Ramadhan?

Sai tace: "Manzon Allah (S.A.W) baya wuce raka'a goma sha ɗaya a Ramadhan ko waninsa.". Bukhari ne ya ruwaito[8] Kuma Nana Aisha taci gaba da cewa: Kar a tambayi irin kyan sallar wajen (kyakkyawan) ruku'u, da Sujjada, kuma yakan daɗe har kafafunsa su kumbura. Saboda haka duk wanda zai taƙaita akan raka'a goma sha daya, to ya kyautata sallar wajen koyi da Manzon Allah (S.A.W) wajen tsawaita ruku'u da sujjada da tsayuwa.

**Tambaya:** SHIN AKWAI BANBANCI TSAKANIN SALLAR ASHAM DA TAHAJJUDI, DA KIYAMULLAILI?

**Amsa**:- Duk nafilar da akayi bayan sallar Isha'i, ana iya kiranta asham, ko tahajjudi ko kiyamullaili.

Amma akwai wasu malamai da suke ganin ba'a kiran nafila tahajjudi sai wadda akayi bayan an tashi daga bacci, sai dai wannan ijtihadinsu ne kawai.

**Tambaya:** IDAN MUTUM BASHI DA HADDA ZAI IYA ƊAUKAN AL'ƘUR'ANI YAYI WA MUTANE LIMANCI?

**Amsa**:- Na'am, domin Asar ya tabbata daga Nana Aisha cewa: "tana gabatar da bawanta (Zakwan) yana duba Alƙur'ani yana musu limanci a sallar tarawihi"[9].

Amma babu wani dalili akan mamu ya rinka duba Ƙur'ani yana bin liman, wannan wasane a cikin sallah.

**Tambaya:** MENENE HUKUNCIN AL'ƘUNUTI A KOWANE WUTURI NA SALLAR TARAWIHI?

(8) Bukhari K = 21, B = 1, H = 1213

(9) Bukhari K = 10, B = 54

**Amsa**:- Yin ƙunuti a cikin wuturi ya tabbata daga Manzon Allah (S.A.W) a Ramadhan ko waninsa, amma a keɓance Ƙunuti a cikin Wutiri a Ramadhana kawai, musamman goman ƙarshe, wannan bai tabbata daga Manzon Allah ba, ko magabata na ƙwarai, amma za'a iya yi wani lokaci wani lokaci kuma a huta.

* Akwai ƙarin bayani akan wannan mas'alar wanda zamuyi nan gaba In Sha Allah.

**Tambaya:** MENENE I'TIKAFI?

**Amsa**:- Iitikafi ma'anar sa a larabci itace, Lizimtar wani Abu, da tsare kai. Amma ma'anarsa a shariah, itace, lizimtar masallaci ga mutumin daya kaɓance kansa a wata siffa keɓantacciya don yin ibadah. I'tikafi ya tabbata a cikin littafin Allah da Sunnar Manzon Allah da Ijma'in Malamai.

**Tambaya:** AINA AKE YIN I'TIKAFI?

**Amsa**:- Ana yin Iitikafi a ɗakin maƙdisi, da sauran masallatai a bisa zance mafi rinjaye. Saboda faɗin Allah: Kada ku kusance su (Iyalanku) alhali kuna masu Iitikafi a masallatai. Kuma imamul Bukhari ya buɗe babin Iitikafi da cewa: "Iitikafi a dukkanin masallatai" sai kuma ya kafa hujja da ayar da ta gabata.

Hafiz ibn Hajar yace anayin I'tikafi a dukkanin masallatai ba tare da keɓance wasu masallatai ba, kuma yaci gaba da cewa jamhurun malamai sun tafi akan zaa iya yin I'tikafi a kowane masallaci. Sai dai Imamu Shafi'i da wasu malamai sunce ana son (mustahabbi) wanda Juma'a ta wajaba a kansa yayi Iitikafinsa a masallacin Juma'a.

Amma Huzaifa ibn Yamani sahabin Manzon Allah (S.A.W) yace ba'a yin I'tikafi sai a masallatai guda uku;

Adda'u yace ba'a I'tikafi sai a masallacin Makka da Madinah;

Saidu bn Musayyib yace baa I'tikafi sai a masallacin Madinah[10].

Amma Hafizu ya danganta hadisin zuwa ga Manzon Allah (S.A.W), kuma Sheikh Albani ya inganta hadisin kuma yayi raddi ga waɗanda suke ganin cewa hadisin mauƙufi ne. Wannan hadisin shine dalilin Sheikh Albani akan cewa baa yin Iitikafi sai a masallatai guda uku (Masallacin Ka'abah, da Masallacin Manzon Allah (S.A.W), da Masallacin Baitil Maƙdisi)[11].

(10) Fathul Bari 4/319

(11) Silsilatul a hadisussahiha (1/667) kashi na shida bugu na ƙarshe maktabatu darul ma'arif Riyadh.

Amma wasu magabata daga cikin sahabbai sun ce Huzaifa yayi wahami daga cikin su akwai Abdullahi bn Mas'ud sahabin Manzon Allah (S.A.W).

Domin Huzaifa ya ga almajiran ibn Mas'ud suna Iitikafi a tsakanin gidan Abdullahi bn Mas'ud da gidan Abu Musal ash ari sai yace bazaka hanasu ba? Hakika kasan Manzon Allah (S.A.W) yace: "Ba a yin Iitikafi sai a masallatai guda uku, sai ibn Mas'ud yace:

Watakila ka manta su kuma sun kiyaye, ko kuma kayi kuskure. Su kuma sun yi dai dai[12].

Kuma kowa dai yasan Abdullahi bn Mas'ud wajen tsananin riƙo da sunnar Manzon Allah (S.A.W) amma duk da haka bai hana almajiransa yin Iitikafin ba, domin yana ganin watakila Huzaifa yayi wahamine ko ya manta.

Abisa waɗannan dalilai da suka gabata, duk wanda yake ganin cewa Huzaifa yayi wahami, kamar yadda Abdullahi bn Mas'ud Sahabin Manzon Allah (S.A.W) yayi nuni, to zai iya yin Iitikafi a kowane masallaci ba tare da ƙa'ida ba.

Hakanan duk wanda yake ganin cewa Khuzaifa bai yi wahami ba, kuma hadisinsa ya inganta, to sai ya taƙaita I'tikafinsa a masallatan nan guda uku.

Saboda haka muna jan hankalin ɗaliban Ilmi musamman waɗanda suketa jayayya ko kafirta juna akan wannan mas'ala da suji tsoron Allah su san cewa wannan mas'alace ta ilmi kuma akwai saɓanin magabata a kanta.

**Tambaya:** YAUSHE AKE SHIGA I'TIKAFI?

**Amsa**:- Ana shiga I'tikafi bayan Sallar Asuba domin hadisi ya tabbata daga Nana Aisha yardar Allah ta tabbata a gareta tace: "Idan Manzon Allah (S.A.W) yayi sallar asuba sai ya shiga gurin I'tikafinsa. Bukhari da Muslim ne suka ruwaito[13].

Manzon Allah (S.A.W) yana shiga Iitikafinsa a daren ashirin da ɗaya bayan yayi sallar asuba. Amma waɗansu malamai suna ganin cewa mai I'tikafi zai shiga masallaci kafin ketowar Alfijir. Kuma bayan yayi sallar asuba sai ya shiga wajen da ya tanada domin Iitikafinsa.

Amma mazahabar malikiyya sun fahimci cewa mai Iitikafi zai shiga Iitikafi kafin faduwar rana, bayan yayi sallar asuba sai ya shiga wajen da ya

(12) Al Mukniy Ash Sharhul Kabir na ibn Kudama al Mukaddasi, wanda Dr. Abdullahi Atturki Yayiwa Tahliki Juzi Na (7/577).

(13) Bukhari K = 33, B = 14, H = 2041, da Muslim K = 14, B = 1, H = 1172.

tanada domin I'tikafinsa. Amma sauran malamai irin su Auza'i, da Thauri da Laith, suna ganin mai I'tikafi zai shiga wajen I'tikafinsa da zarar ya gama sallar asuba domin su sun yi amfani da zahirin hadisin ne.

Kuma wannan shine zance mafi rinjaye, saboda lafazin hadisin Muslim ma yana ƙarfafa shi(14).

**Tambaya:** SUWAYE YA KAMATA SUYI I'TIKAFI?

**Amsa**:- I'tikafi sunnar Manzon Allah (S.A.W) ce wadda ta shafi maza da mata, domin Manzon Allah (S.A.W) yayi, kuma iyalansa sun yi, harma matar datake da jinin istahala (Mataccen jini) zata iya yin I'tikafi domin hadisi ya tabbata daga Nana Aisha Allah ya yarda da ita tace: "Wata daga cikin iyalan Manzon Allah (S.A.W) tayi I'ikafi tare dashi kuma ta kasance tana cikin jinin Istihala"(15).

Amma Abin mamaki an manta da wannan sunnar mai albarka, wadda Annabi (S.A.W) ya lizimceta tsawon rayuwarsa, matan sa kuma suka ci gaba da rayata bayansa.

Maimakon Malamai masu kira zuwa sunna su tsaya su rayata, sun bar yara matasa ne kawai sune suke rayata. Ina masoya Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) masu da'awar khalwa?

To ga khalwar Manzon Allah wadda ta tabbata daga mafificin halitta Annabi Muhammad (Sallallahu Alaihi Wasallam), ba khalwar shaiɗanu wadda take haukatar da yara ba.

**Tambaya:** MENENE YA KAMATA MAI I'TIKAFI YA SHAGALTU DASHI?

**Amsa**:- Anfi son mai Iitikafi ya shagaltu da karatun Alƙur'ani, da Zikiri da hailala, da Nafil fili da salatin Annabi (S.A.W). Ba'a son mai I'tikafi ya fita daga cikin masallaci saida larura kamar fitsari ko bayan gida, ko kawar da datti kamar wanka, ko cin abinci ga wanda bai sami wanda zai kawo masa ba.

Yakamata mai I'tikafi ya daina giba da namima da shagala da jin rediyo da surutun banza. Nana Aisha tace: "A Sunnah, mai Iitikafi ba zai jana'iza ba ba zai sadu da iyalansa ba, ba zai rungumesu don sha'awa ba, kuma ba zai fita ba sai larurar da bata da makawa".

---

(14) Mai neman ƙarin bayani sai ya duba Al istizkar na Ibn Abdulla Bar, (10/311) da Sharhin Mushin na Kadhi Iyadh Ikmalul Mu'allim fi Fawaidil Muslim (4/154).

(15) Sahihi Sunanu Abi Dawuda wanda Albani yayi wa tahaliƙi (2/469) hadisi na 2476.

Kuma ba'a I'tikafi sai da Azumi kuma sai a masallacin juma'a[16].

Babu laifi akai wa mai I'tikafi ziyara. Musamman iyalansa, don hadisi ya tabbata iyalan Manzon Allah (S.A.W) sukan kai masa ziyara ya raka su zuwa ƙofa amma baya fita, wasu malamai sun halattawa mai I'tikafi saurаran Ilmi a cikin masallacin da yake I'tikafi, domin Ilmi yana cikin ibadah[17]. Kuma ya kamata mai Iitikafi ya yawaita yin Addu'a musamman dararen da ake sa ran samun daren lailatul ƙadari, saboda burin mai Iitikafi shine dacewa da daren lailatul ƙadari.

Domin Manzon Allah (S.A.W) ya taɓa yin I'tikafi a goman tsakiya, da wahayi yazo masa cewa lailatul ƙadari yana gaba sai ya sake komawa domin ya dace da ita[18].

Mai yin I'tikafi zai iya yin kwana Ashirin, kuma zai iya yin kwana goma ko kwana ɗaya.

Amma abun mamaki yanzu wurin Iitikafi ya zama dandalin surutu, da shagala, da yin labarai, da fita shakatawa a harabar masallaci ba tare da lalura ba, da jayayya, da faɗa a tsakanin mutane da ɗauke ɗauken hotuna, da shiga wajen I'tikafi da mata, da musayar wasiku, duk waɗannan sun saɓawa sunnar Manzon Allah (S.A.W).

**Tambaya:** YAUSHE NE AKE FITA DAGA I'TIKAFI?

**Amsa**:- Iitkafi yana ƙarewa ne daga watan karamar sallah. Amma idan mutum ya tsaya a masallaci, to zaɓinsa ne amma ba I'tikafi yake ba. Kodayake mazahabar malikiyya sun fi son yayi hakan, amma suma basuce I'tikafi yake yi ba.

**Tambaya:** YAUSHE AKE SA RAI DA DAREN LAILATUL ƘADARI?

**Amsa**:- Ana sa rai da daren lailatul ƙadari a dararen 21, 23, 25, 27 da 29. Domin hadisi ya tabbata daga Abdullahi bin Umar (RA) yace, Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Ku nemi daren lailatul ƙadari a wutiri na goman ƙarshe"[19]. Amma hadisai da yawa sun ƙarfafa daren 27. An karɓo wani hadisin daga Abdullahi bin Umar (RA) yace: Manzon Allah (SAW) yace:

---

(16) Abu Dawuda ne ya ruwaito shi mauƙufi akan Nana Aisha, Hafiz bn Hajar ya Ingantashi kuma Albani yace hadisi ne hasanun sahih, sahihisunan Abu Dawuda na Albani (Hadisi na 2473).

(17) Duba Sharhin Muslim na Kadi Iyad 4/157.

(18) Bukhari

(19) Bukhari

"Kuyi ƙirga don lailatul ƙadari a bakwai na ƙarshe"[20].

**Tambaya:** SHIN GASKIYANE A DAREN LAILATUL ƘADARI ANA GANIN KOMAI YANA YIN SUJADA, KAMAR BISHIYOYI DA GIDAJE HARMA MUTUM YA RINKA HANGO KA'ABA DAGA DUK INDA YAKE?

**Amsa**:- Wannan bai tabbata ba daga Manzon Allah (SAW) ko magabata na ƙwarai; ijtihadin wasu mutane ne ba tare da wani dalili na shari'a ba. Amma ya tabbata wasu daga cikin sahabbai "An nuna masu a mafarki cewar daren lailatul ƙadari yana cikin bakwai na ƙarshe[21](3)" Wannan hadisin ya nuna cewar an nuna masu ranar ne amma ba wani abu suka gani ba.

Amma ana ganin alamomin daren lailatul ƙadari kamar yadda Annabi (SAW) ya bada labari cewar

(3) Muslim (Sharhin Khadi Iyad, 1165)

"Ranar daren lailatul ƙadari takan fita bata yin zafi(1). Kuma Manzon Allah (SAW) yace: "A cikinku wa zai tuna daren da wata ya fito kamar rabin akushi? Ana faɗin daren lailatul ƙadari sai Annabi (SAW) ya faɗi haka"(2).

, alhali yana mai cike da baƙin ciki. Yana ɓoyewa daga mutane domin munin abin da aka yi masa bushara da shi. Shin zai riƙe shi a kan wulakanci, ko zai turbuɗe shi a cikin turɓaya? To, abin da suke hukumtawa ya munana".(Surar Nahali : 16:58-59)

"Kuma kada ku kashe 'ya'yayenku domin tsoron talauci. Mu ne ke arzurta su, su da ku. Lalle ne kashe su ya kasance kuskure babba". (Surar Isra'i : 17: 31)

"Kuma idan wanda aka turbuɗe ta da rai aka tambaye ta : saboda wane laifi ne aka kashe ta". (Surar Takawiri : 81: 8-9)

Kana kuma an ruwaito Annabin rahama (s.a.w) yana cewa:

"Wata rana wani mutum mai suna Qais bin Asim al-Tamimi, ya zo wajen Manzon Allah (s) ya ce: " a lokacin Jahiliyya na kasance na bisne 'ya'yayena mata guda takwas....[1]" .

Hakika za'a iya bayyana zamanin Jahiliyya na larabawa kafin zuwan Musulunci kamar haka :-

(20) Muslim (206)

(21)

“An kasance ana bisne ‘ya’yaye mata cikin mummunan yanayi; a kan bisne jariri da rai ! sukan yi amfani da hanyoyi daban-daban wajen gudanar da wannan al’ada. Idan aka haifawa ɗaya daga cikinsu ɗiya mace, to sukan bar ta har na tsawon shekaru shida. Daga nan sai mahaifinta ya yi umrnin da a yi mata ado a shafa mata turare da ƙaryar cewa zai kaita wurin danginta ne ! To amma a dai-dai lokacin an riga an tona mata wani rami cikin rairayin sahara. A lokacin da suka isa sai mahaifin nata ya ce mata ta leka ramin, nan take sai ya tura ta cikinsa , kana ya rufe ta da ƙasa!

Wasu kuwa sukan yi amfani da wannan hanyar :- Wato lokacin da naƙuda ta kama mace sai ta je ta zauna a bakin wani rami (da aka riga aka tona). Idan har ta ga abin da ta haifa mace ce, sai ta jefa ta cikin ramin, kana ta rufe ta da kasa. Idan kuwa namiji ne, sai ta ɗauke shi zuwa gida !

“ Kana wadanda ba sa so su bisne ‘ya’yayen nasu mata, sai su barsu cikin wulakanci har su kai shekarun da za su iya yin kiwo, to sai a sanya musu riguna masu gashi a tura su rairayin sahara don kiwon raƙuma !

“Sannan waɗanda ba sa so su tura ta kiwo, sai su yi amfani da wasu muggan hanyoyi don wulakanta ta. Misali idan yarinyar ta girma ta isa aure sai a yi mata aure, idan mijin nata ya mutu sai uban (waliyin) nata ya zo ya sanya mata wasu irin tufafi na musamman wadanda ke nuna cewa ba ta da wani ‘yancin yin aure ba tare da yardar uban nata ba. Ta haka ne za a tilasta mata yin aure ba tare da sonta ba ! To idan shi uban nata ba ya son ya aure ta, to za ta zauna nan a ɗaure har ta mutu, kana kuma sai ya gaje ta. Idan kuwa har tana son ta fanshi kanta daga irin wannan hali, dole ne sai ta bayar da wasu kuɗaɗe don ta ‘yantar da kanta.

“ Wasu kuwa sukan ‘yantar da matan, amma fa da sharaɗin ba za su taɓa yin aure ba sai dai da izinin waliyin nasu, ko kuma dole ne ta biya diyya. Wasu kuwa sukan ajiye bazawarai waɗanda mazajensu suka mutu har sai wani daga cikin ‘ya’yayensu ƙanana ya girma kafin su aurar masa da ita.

“Dangane da mace marainiya kuwa, sukan ajiye ta ne a wajensu kana su hana ta aure da burin cewa za su aure ta lokacin da matayensu suka mutu, ko kuma su sanya ta ta auri ɗaya daga cikin ‘ya’yayensu don saboda su sami dukiyarta....(1)

Su kuwa Girkawa, suna ganin mace a matsayin wata doluwar halitta ce da bata da wani ‘yanci gudanar da duk wani al’amari.

Hatta wasu daga cikin falasafofin ƙasar Girka sun ɗauki kulle mace a cikin gida, kamar sanya ta cikin kurkuku ne. Wani mashahurin mai hikima